

Gata nan gata nan ku!

An yi wata yarinya mai suna Asabe.

Asabe yarinya ce mai kwaɗayi.

Wata rana an daura

auren Asabe.

An kama hanyar kai

Asabe gidan miji.

Asabe ta ga tukunyar

nama a hanya.



Asabe tana son cin naman.

Iyayen Asabe sun hana ta cin naman.

Asabe ta rasa yanda za ta yi.







Bayan tafiya ta yi nisa.

Sai Asabe ta ce ta manta zanenta.

Iyayenta suka ce ba damowa.

Za su saya mata wani zani.

Asabe ta sake tunani.

Asabe ta ce ta manta akwatinta.

Iyayenta sun ce ta bari.

Za su saya mata wani akwati.





Asabe tana son ta ci nama.

Asabe ta ce ta manta ranta.

Iyayenta sun ce ta je ta ɗauko.



Asabe ta koma wurin

tukunyar nama.

Asabe ta buɗe ta ci

nama.

Naman Dodanniya ne

Asabe ta ci.

Asabe ta dawo wurin iyayenta.

Asabe bata iya magana.

Harshen Asabe ya yi dogo.

Harshenta na lilo a bakinta.

